**KOMAI NISAN JIFA…..**

**EPISODE 22**

**Characters**

Husseini

Laraba

Lantana

Inna

Hanna

Kande

**Scene I**

*NORTHERN KADUNA, HEALTH CENTRE*

1. **MUSIC:** **THEME MUSIC**
2. **SFX:** **HOSPITAL AMBIENCE WITH MURMURING, SOUND OF BABIES CRYING.**
3. **LARABA:** **(CALLING OUT)** Wa ke biye? Wa ya kamata ya siga?
4. **SFX:** **(OFF MIC) SLOW HEAVY FOOTSTEPS APPROACH.**
5. **HUSSEINI:** **(WEAKLY, OUT OF BREATH COMING ON-MIC)** Nas Laraba…
6. **LARABA:** **(SHOCKED)** Malan Husseini! Menene? Lafiya kuwa? Shigo ka zauna.
7. **SFX:** **CHAIR CREAKS AS HUSSEINI SITS DOWN**
8. **HUSSEINI:** **(WEAKLY)** Nas Laraba, ban gane yadda jiki na ke yi ba. *K*irji na …

9. **SFX:** <u>**SOUND OF CHAIR SCRAPING AS LARABA RISES AND FOOTSTEPS AS SHE APPROACHES HUSSEINI**</u>

10. **LARABA:** Ba komai Malan Husseini. Bari na dub aka na auna hauhawar jininka.

11. **HUSSEINI**: **(BREATHING HEAVILY)** Nagode Nas Laraba.

12. **LARABA:** Malan Husseini, daman kana shan wata magani ne?

13. **HUSSEINI**: Eh, na sha wasu magungunar sa barci domin ina ta samun matsalar rashin barci.

14. **LARABA:** Ka samu ka magance wannan matsalar bayan ka sha magungunan?

15. **HUSSEINI**: Babu fa, ban samu wani sau*k*i ba. Sai kuma yau da safe da nake shago sai *k*irji na ya fara yi mun ciwo, na kasa jan numfashi kamar yadda ya kamata, shi yasa na zo. **(PANICKING, BREATHING HEAVILY)**

16. **LARABA:** **(WORRIEDLY)** Don Allah Malan Husseini, ka kwantar da hankalinka ka ji? Ka kwantar da hankalinka komai zai daidaita.

17. **HUSSEINI**: **(BREATHING DEEPLY, SLIGHTLY CALMER)** Nagode Nas Laraba, zan yi *k*o*k*ari.

18. **LARABA:** (**SIGHS**) Mal. Husseini, a yanayin da hauhawar jininka yake zan tura ka zuwa babbar asibiti domin su *k*ara duba ka.

19. **HUSSEINI**: (**ALARMED**) Me yasa zaki tura ni zuwa babbar asibiti? Matsala na babba ce ko? Ko zan mutu ne?

20. **LARABA:** **(SOOTHINGLY)** Malan Husseini, ka kwantar da hankalinka. Baka ga na zauna ina yi maka magana a nitse ba? Komai zai daidaita.

21. **HUSSEINI:** Toh me zai sa na je babbar asibiti?

22. **LARABA:** Zan tura ka ne saboda kamar yadda ka sani, Dr. Daoud baya asibiti yau. Kuma saboda yanayin hauhawar jininka da bugun zuciyar ka, da kuma yadda kake samun matsalar rashin barci, ina son ka ga likita domin a nemi magani.

23. **HUSSEINI:** Gaskiya Nas, abubuwa sunyi mun yawa ne, kuma yana shafar lafiyar jiki na. Bana iya cin abinci ko barci kamar yadda ya kamata, kuma *k*irji na na yawan ciwo.

24. **LARABA:** Ah Malan Husseini, ai da ka so asibiti tuntuni. Amma ba komai. Bari na nemo maka tasi da zai kai ka babbar asibitin. Ina son ka je yanzu.

25. **HUSSEINI:** Nagode Nas Laraba, amma kar ki damu, zan iya neman tasi da kai na. Ina *d*an jin sau*k*i. Zan je yanzu.

**26. SFX**: **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**<u>SCENE 2</u>**

*NORTHERN KADUNA: HAJIYA INNA'S COMPOUND*

**27. SFX:** **<u>SOUNDS OF CHICKENS AND OTHER DOMESTIC ANIMALS</u>**

28. **LANTANA:** **(OFF MIC, CALLING OUT)** Assalamu alaikum! Akwai mutun a gida?

29. **INNA:** **(ON MIC)** Wa'alikumus salam …. Wanene?

30. **LANTANA:** Ni ce. Sunana Lantana. Na zo ganin Laraba. Don Allah tana nan?

31. **INNA:** Eyah ta je wajen aiki. Nice Inna, uwar *d*akinta. Ki shigo ki jira ta. Ta kusa dawowa.

32. **LANTANA:** Toh ba komai Hajiya Inna. Zan jira ta.

33. **SFX:** **SOUND OF A CHAIR SCRAPING THE FLOOR AS LANTANA SITS**

34. **INNA:** Toh Hajiya Lantana, bari na kawo miki abu ki sha.

35. **LANTANA:** A'a, Hajiya Inna, nagode. Ba komai.

36. **INNA:** **(CURIOUS)** Ke *k*awar Laraba ce, ko kuma gwaggonta ne? Ta yi watanni a nan amma ban ta*b*a ganin ki kin ziyarce ta ba.

37. **LANTANA:** A'a, ni mahaifiyarta ce, na zo ne daga Zaria domin na gan ta.

38. **INNA:** **(SURPRISED)** Mahaifiyarta? Malama Lantana, kin tabbata?

39. **LANTANA:** **(BEWILDERED)** Ah Hajiya Inna, me yasa kike mamakin cewa na ce ni mahaifiyar Laraba ce?

40. **INNA:** **(SUSPICIOUSLY)** Na yi mamaki ne domin tabbas Laraba ta gaya mun wai ita bata da uwa, bata da uba.

41. **LANTANA:** **(CHUCKLES SADLY)** Ta fa*d*i gaskiya. Kin gani, ni kishiyar mahaifiyarta ce. Bayan maigidanmu da mahaifiyarta suka rasu, nice na ri*k*e ta.

42. **INNA:** Allah Sarki! **(PAUSES)** Ai da Laraba ta gaya mun cewa zaki zo. Da na sani da na dafa miki abinci. Yi ha*k*uri fa Hajiya Lantana. Marhaban.

43. **LANTANA**: Ah Hajiya Inna, nagode. Laraba bata san zan zo ba. Tayi ta ce mini kar na damu da ziyartan ta.

44. **INNA**: Da gaske?

45. **LANTANA**: Eh Hajiya. Na yanke shawara ne kawai na zo yau domin na ja kunnen Laraba.

46. **INNA:** **(SURPRISED)** Ah amma Laraba yarinya ne mai hankali Malama Lantana. Me zai sa ki ja mata kunne?

47. **LANTANA**: Na yarda Inna. Yadda na ji muryar Laraba ne a waya ya dame ni. Da na kira *k*awarta Hannah ta gaya mun dalilin ba*k*in cikinta, sai na ce bari na zo na ganta kawai.

48. **INNA:** Ah tayi sa'an samun ki Lantana. Amma har yanzu ina mamaki cewa baki ta*b*a zuwa ba.

49. **LANTANA:** Ehn Hajiya Inna, abun da nake fa*d*i kenan. Na so na zo tuntuni amma 'ya ta Laraba bata son tarihinta ya shigo Kaduna. Ina miki godiya da kike ta kula da ita har tsawon wannan lokacin.

50. **INNA**: Haba, babu komai. Na *d*auka Laraba tamkar 'ya ta **(CURIOUSLY)** amma ban gane abun da kika ce batun tarihinta ba. Akwai abun da take *b*oye mana ne?

51. **LANTANA:** Laraba ta ga abubuwa marasa da*d*i a rayuwarta, wanda yasa take gani kamar bata da sa'a …

52. **INNA:** Tsaya fa Lantana, ina fatan ba don ta rasa iyayenta bane ba?

53. **LANTANA:** Toh Hajiya, ta rasa iyayenta da 'yanuwanta maza guda biyu a cikin gobara, ita ce kawai ta rayu bayan gobarar.

54. **INNA:** **(SHOCKED)** Kai! Allah Sarki!

55. **LANTANA:** Sai kuma a shekarar da ta wuce, saurayinta Jallo, a lokacin da zasu zo tare da ‘yanuwansa su nemi aurenta suka samu mumunar ha*d*arin mota, duk suka hallaka!

56. **INNA:** *Subhanallah!* Ban sani ba! Allah Sarki! Shi yasa ta cika nisantar da kanta!

57. **LANTANA:** Eh, amma ita ta yarda cewa laifin ta ne duk wannan ke faruwa, saboda haka take zubar da damar ta samu zaman lafiya da wani likita haka.

58. **INNAH**: Kina nufin wannan Dr. Daoud dake zuwa da ya gan ta?

59. **LANTANA:** Eh Hajiya Inna, Shine.

60. **INNA:** Amma fa kamar Laraba na son sa da, sai dai ya daina zuwa.

61. **LANTANA**: Dalilin kenan da na zo, domin na ja mata kunne akan *k*in Daoud da take yi.

62. **INNA:** **(WORRIEDLY)** Ki? Ana ganin sa da daraja a wannan al’umma fa. Me yasa zata *k*i sa? Yaran yanzu ma, kai!

63. **LANTANA**: Tana tunanin cewa tana da rashin sa’a, wai bata son wannan dake nemanta ya rasa ransa. Shi yasa take *k*in sa.

64. **INNA:** Hmmm. Yau ga wata al’amari. Ina fata zaki iya shawo kan Laraba, saboda bai kamata ta zubar da damar nan na moriyar rayuwarta.

65. **LANTANA**: **(SIGHS)** Na fa yarda da maganar ki Innah. Muna nan muna fatar alkhairi.

66. **INNAH:** **(TEASINGLY)** Kin ga Lantana, kar ki damu, yau kin damu domin kina son ganinta a *d*akin mijinta, gobe zaki ta yin *k*o*k*arin taimaka mata ta bada tazzara tsakanin

haihuwa kamar yadda ya kamata! Komai zai daidaitu *k*awa ta!

**67. MUSIC:** **BRIDGE MUSIC**

**SCENE 3**

*NORTHERN KADUNA: HAJIYA INNA'S COMPUND*

68. **SFX:** **SOUND OF ROOM DOOR BEING UNLOCKED**

69. **LANTANA:** *Wa'alaikumus salam*, Laraba.

70. **LARABA:** **(SURPRISED)** Ah Hajiya Lantana, yaya na gan ki a nan? Yaushe kika sauka?

71. **LANTANA**: Nayi kamar awa *d*aya da isowa, Hajiya Inna ce ta taimaka mun da wajen zama na jira dawowanki. Na zo ne naji da kaina dalilin da kike cikin ba*k*in ciki, ban ji da*d*in yadda naji muryarki ba.

72. **LARABA:** Eyah! Ai da baki dame kanki ba, ina nan lafiya, babu abun dake damu na.

73. **LANTANA**: (**CUTS IN)** Kar ki gaya mun wannan Laraba, domin na riga nayi magana tare da Hannah tun daga Zaria kuma ta gaya mun cewa kin zubar da saurayinki Dr. Daoud.

74. **LARABA:** Amma Mama, da baki kira Hannah ba domin a yanzu tana da damuwa kala-kala.

75. **LANTANA**: **(APOLOGETIC)** Ta yaya zan san haka Laraba, bayan kin *k*i kiyi mun magana.

76. **LARABA:** **(TEARFULLY)** Mama, abun da *d*an wuya. Kin ga, na riga nayi wa Daoud kwatancen gidan Kawu Abdul, sai kuma wani abu ya taso.

77. **LANTANA**: **(GENTLY)** Me ya taso … don Allah ki gaya mini. Kar ki manta cewa ni mamanki ce kuma ina neman cigabanki.

78. **LARABA:** Na sani. Ya bani labarin iyalinsa da yadda ya rasa matarsa da yaransu a ha*d*arin mota.

79. **LANTANA**: **(SHOCKED)** Eyah! Ina tausaya masa. Amma abun da ban gane ba shine me yasa zaki *k*i Dr. Daoud akan abun da ya gaya miki?

80. **LARABA:** Ina ganin cewa rashin sa'an Dr. Daoud ha*d*e da nawa zai kawo babbar rashin sa'a in muna tare.

81. **LANTANA**: Don Allah Laraba ki bar wannan shirmen, ki manta da baya ki fuskanci gaba. Don Allah Laraba ki cigaba da rayuwarki.

82. **LARABA:** Na yarda cewa ina da rashin sa'a, shi yasa bana son na saka ran Dr. Daoud da yaran da zamu samu a ha*d*ari.

83. **LANTANA**: Laraba, ke yarinya ce mai wayo. Da ace *k*awarki ce Hannah a cikin wannan hali, wani shawara ne zaki bata? Ta zubar da damar samun farin ciki a rayuwarta?

84. **LARABA**: A'a Mama. Zan gaya mata cewa abun da ya faru ba laifinta bane.

85. **LANTANA**: Ha*k*i*k*a. Don Allah kiyi nazari Laraba. Eh! Kiyi mini al*k*awari.

86. **LARABA:** Toh, nayi al*k*awarin zan yi tunani akan abun da kika fa*d*a Mama. Kuma ina godiya sosai da zuwanki.

87. **LANTANA**: Toh Laraba. Na gaya miki duk abun da nake son na gaya miki. Ina fata ba da da*d*ewa ba kawunki zai gaya mun cewa Dr. Daoud da mutanensa sun je sun gan shi.

**88. MUSIC:** **BRIDGE MUSIC**

**SCENE 4**

*NORTHERN KADUNA: KANDE'S HOUSE*

| | |
|---|---|
| **89. SFX:** | **SOUND OF A DOOR BEING OPENED AND CLOSED** |
| 90. **KANDE:** | **(COMING ON MIC)** Hannah? |
| 91. **HANNAH:** | **(SOBBING)** Na'am Mama? |
| 92. **KANDE:** | Hannah ki kwantar da hankalinki. Bai kamata kina tsaya haka ba, eh? |
| 93. **HANNAH:** | **(SNIFFLING)** Na'am Mama? |
| 94. **KANDE:** | Hannah, maigidanki Danjuma na waje yana jiranki. |
| 95. **HANNAH:** | **(SOUNDING DEPRESSED AND SAD)** Don Allah Mama ki gaya mishi ya *k*yale ni … ban so nayi masa magana. |
| 96. **KANDE:** | **(PLEADINGLY)** Hannah ina ganin ya kamata ki saurari Danjuma, ki ji yadda abun yake daga nashi gefen. |
| 97. **HANNAH**: | Don Allah Mama ki *k*yale ni. Bani da abun da zan ce wa Danjuma. |
| 98. **KANDE**: | Hannah kar kiyi taurin zuciya, kiyi ha*k*uri. |
| 99. **HANNAH**: | Mama ba zan ganshi ba, domin bamu da abun da zamu tattauna tare dashi. Na san abun da na gani, kuma idanuwa na baza su yi mun *k*arya ba. |
| 100. **KANDE:** | **(UNCERTAINLY)** Amma Hannah kin tabbata cewa abun da kika gani ko ji gaskiya ne? Ina tsammanin akwai wata kuskure a cikin maganar. |
| 101. **HANNAH**: | **(INCREDELOUS)** Mama, kina shakkar magana na ne? |

102. **KANDE:** Ba wai ina shakkan abun da kika gaya mini ne bane, amma bayan nayi magana tare da Danjuma, kuma ganin yadda abun ya dame shi ya rikita shi, ban da tabbas kuma.

103. **HANNAH**: **(SOUNDING HURT)** Mama kina cewa kin yarda da maganan shi? *K*arya ne yake yi.

104. **KANDE:** Na yarda da magananansa mana, kuma kar ki manta cewa Danjuma ba ma*k*aryaci bane.

105. **HANNAH**: **(UPSET)** Yanzu Mama, kina kira na ma*k*aryaciya kenan ko? Cewa nice nake *k*arya???

106. **KANDE**: **(GENTLY)** A'a Hannah, abun mamaki shine na yarda da magananku ku biyu. Ina ganin cewa akwai dalilin da kika ga abun da kike tsammanin kin gani.

107. **HANNAH**: Babu wata hujja da zai sa Danjuma ya sa ni kunya, ya ci amanar soyayya da amincin dake tsakaninmu, ba zan ta*b*a yafe mishi ba.

108. **KANDE:** Hannah, ki saurari Danjuma. Yana waje yana jiranki, ki saurare shi domin yayi miki bayani.

**109. MUSIC:** **<u>THEME MUSIC</u>**